*16.* Kuma Ni, Ina mayar da kaidi (gare su) kamar yadda suke ƙulla kaidi,

وَأَكِيدُ كَيْدًا ﴿١٦﴾

*17.* Sabõda haka, ka yi wa kãfirai jinkiri, ka dãkata musu, sannu-sannu.

فَمَهِّلِ ٱلْكَٰفِرِينَ أَمْهِلْهُمْ رُوَيْدًۢا ﴿١٧﴾

## SŨRATUL A'ALÃ سُورَةُ الأَعْلَىٰ

Tana karantar da cewa rãyarwa da matarwa ga hannun Allah suke, sũ kuma nau'i-nau'i ne.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Ka tsarkake sũnan Ubangijinka Mafi ɗaukaka,

سَبِّحِ ٱسْمَ رَبِّكَ ٱلْأَعْلَى ﴿١﴾

*2.* Wanda Yã yi halitta sa'an nan Ya daidaita abin halittar,

ٱلَّذِى خَلَقَ فَسَوَّىٰ ﴿٢﴾

*3.* Kuma Wanda Ya ƙaddara (abin da Ya so) sannan Ya shiryar, (da mutum ga hanyar alhẽri da ta sharri),

وَٱلَّذِى قَدَّرَ فَهَدَىٰ ﴿٣﴾

*4.* Kuma Wanda Ya fitar da makiyãyã,

وَٱلَّذِىٓ أَخْرَجَ ٱلْمَرْعَىٰ ﴿٤﴾

*5.* Sa'an nan Ya mayar da ita ƙeƙasassa, baƙa.

فَجَعَلَهُۥ غُثَآءً أَحْوَىٰ ﴿٥﴾

*6.* Za mu karantar da kai (Alƙur'ãni) sabõda haka bã zã ka mantã (shi) ba.

سَنُقْرِئُكَ فَلَا تَنسَىٰٓ ﴿٦﴾

*7.* Fãce abin da Allah Ya so, lalle ne Shi (Allah) Ya san bayyane da abin da yake ɓõye.

إِلَّا مَا شَاءَ اللَّهُ ۚ إِنَّهُ يَعْلَمُ الْجَهْرَ وَمَا يَخْفَىٰ ﴿٧﴾

*8.* Kuma za Mu sauƙaƙe maka (al'amari) zuwa ga (Shari'a) mai sauƙi.

وَنُيَسِّرُكَ لِلْيُسْرَىٰ ﴿٨﴾

*9.* Sabõda haka, ka tunãtar, idan tunatarwa zã ta yi amfãni.

فَذَكِّرْ إِن نَّفَعَتِ الذِّكْرَىٰ ﴿٩﴾

*10.* Wanda yake tsõron (Allah) zai tuna.

سَيَذَّكَّرُ مَن يَخْشَىٰ ﴿١٠﴾

*11.* Kuma shaƙiyyi, zai nisance ta,

وَيَتَجَنَّبُهَا الْأَشْقَى ﴿١١﴾

*12.* Wanda zai shiga wutar da tã fi girma,

الَّذِي يَصْلَى النَّارَ الْكُبْرَىٰ ﴿١٢﴾

*13.* Sa'an nan bã zai mutu ba a cikinta, kuma bã zai rãyu ba,

ثُمَّ لَا يَمُوتُ فِيهَا وَلَا يَحْيَىٰ ﴿١٣﴾

*14.* Lalle ne wanda ya tsarkaka (da imãni) yã sãmu babban rabo.

قَدْ أَفْلَحَ مَن تَزَكَّىٰ ﴿١٤﴾

*15.* Kuma ya ambaci sũnan[1] Ubangijinsa, sa'an nan yã yi salla.

وَذَكَرَ اسْمَ رَبِّهِ فَصَلَّىٰ ﴿١٥﴾

*16.* Ba haka ba! Kunã zãɓin rãyuwa ta kusa (dũniya)[2]

بَلْ تُؤْثِرُونَ الْحَيَاةَ الدُّنْيَا ﴿١٦﴾

*17.* Alhãli Lãhira ita ce mafi alheri kuma mafi wanzuwa,

وَالْآخِرَةُ خَيْرٌ وَأَبْقَىٰ ﴿١٧﴾

*18.* Lalle ne wannan[3] yanã a cikin litaffan farko.

إِنَّ هَٰذَا لَفِي الصُّحُفِ الْأُولَىٰ ﴿١٨﴾

*19.* Littaffan Ibrãhĩm da Mũsã.

صُحُفِ إِبْرَاهِيمَ وَمُوسَىٰ ﴿١٩﴾

---

(1) Ya ambaci sũnan Allah ga ayyukansa duka, ya yi sallolin nan biyar da sauran ibãdõdi duka.

(2) Rayuwa iri biyu ce, ta dũniya da ta Lãhira.

(3) Kamanta rãyuwar ciyãwa da rãyar da ummiyyi da ilmi bãbu mantuwa, da rãyar da mãtattu cikin sa'ãda ko cikin shaƙãwa yana cikin litaffan farko.